JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA 17 Rajab, 1443
MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI 18 Febrairu, 2022

(1)

## ISRA'I DA MI'IRAJI DA MANYAN AYOYIN ALLAH

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Allah ya tsarkaka ga barin duk wani abu da bai dace da shi ba, shi ne wanda ya yi tafiyar dare da bawansa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) a cikin wani yanki na dare daga Masallacin Harami na Makka, zuwa Masallacin al- Aƙsa da yake a garin Baitul Maƙdisi, wanda Allah ya yi ya yi wa mazauna wurin albarka a cikin abincinsu, saboda mu nuna masa wasu daga cikin ayoyinmu da suke ɗauke da cikakkun hujjoji kuma gamsassu akan kaɗaitakarmu da girman ikonmu, lallai Allah shi kaɗai shi ne mai yawan ji da gani)** [al- Isra'i: 1], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai tafiyar Isra'i da Mi'iraji mu'ujizar Allah ce mai girma, da take nuni zuwa ga cikakken ikon Allah Maɗaukakin Sarki, lallai shi mai girma da buwaya shi ne mahalicci sabubba da abubuwan da sabubba suke haifarwa, duk abin da yake na mamaki a cikin rayuwa da duniyar mutane, to ba abin mamaki da al'ajabi ba ne a wurin Allah mai girma da buwaya, shi al'amarin kaman yanda Allah mai girma ya faɗa ne cewa: **(Ai da ma can dukan al'amarinsa idan ya so wani abu cewa da shi yake yi: kasance, take sai ya kasance)** [Yasin: 82].

Lallai Allah Mai girma da buwaya ya ƙarfafi masoyinsa, kuma zaɓaɓɓensa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da wannan tafiyar, inda ya ɗaukaka shi daga duniyar ƙasa, zuwa duniyar sama, ya sadar da shi har zuwa Sidratul muntaha, saboda ya nuna masa manyan ayoyinsa, da abubwan mamakinsa masu girma.

A cikin waɗannan manyan ayoyin akwai waɗanda muka sani, akwai kuma waɗanda ba mu sani ba, inda Allah mai girma da ɗaukaka ya yi tafiyar dare da Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), tun daga Masallaci mai alfarma "Ka'aba" har zuwa Masjidul Aƙsa, sannan ya hau da shi zuwa sammai maɗaukaka, ya dawo da shi Masjidul Aƙsa, sannan kuma ya dawo da shi Masallaci mai alfarma, duka a dare ɗaya; lallai wannan iko da ƙudura ne na Allah Maɗaukakin Sarki ba wani abu ba.

Lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ga abubuwan ban mamaki na iko da ƙudurar Allah mai girma da ɗaukaka a cikin duniyoyin sammai, Alƙur'ani mai girma yana jawo hankulanmu zuwa ga yin duba zuwa ga manyan ayoyin Allah, Allah yana cewa: **(Da sannu za mu cigaba da nuna masu ayoyinmu a sasannin duniya, da ma a karan kawunansu har sai sun gane cewa lallai shi ɗin ne gaskiya)** [Fusilat: 53].

A cikin waɗannan manyan ayoyin akwai: irin yanda Allah mai girma da buwaya ya hore wa Manzonmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) Buraƙa, (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(An kawo mini Buraƙa, dabba ce fara mai tsawo, tana ajiye kofatonta a inda iya ganinta yake),** lallai wannan babban dalili ne da yake nuni zuwa ga cikakken ikon Allah a cikinta, haka ma a cikin yin haka akwai cikakken

karantarwa ga Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) game da riƙo da sabubba, lallai Allah mai girma da ɗaukaka yana da cikakken ikon ya yi wannan tafiya ta dare da shi ba tare da yin amfani da wani sababi ba.

Haka a cikinsu akwai: Irin yanda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya sadu da Annabawa, da Manzanni, inda a nan ma iko da ƙudurar Allah suka bayyana akan rayawa bayan mutuwa, domin Allah ya raya su ne sabaoda shi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), dukansu suka yi sallah a bayansa a Masjidul Aƙsa, ya kuma haɗu da waɗanda ya haɗu da su a sammai maɗaukaka, dukansu suka yi maraba da shi, suka yi masa addu'a ta alhairi, wannan ya zo ne domin su cika alƙawarin da suka ɗauka wa Allah mai girma da ɗaukaka, a inda Allam Maɗaukakin Sarki yake cewa: **(Ya kai wannan Annabi (SallalLãhu alaiHi wa alihí wa sallam), faɗa masu cewa: lallai Allah ya yi alƙawari da duk wani Annabi da aka saukar masa da littafi, aka kuma ba shi ilimi mai amfani cewa idan wani Manzo da da'awarsa ta yi daidai da da'awarsu ya zo masu, lallai za su yi imani da shi, kuma za su taimake shi... Ya yi alƙawari da kowane Annabi akan haka, suka yi iƙirari da haka, suka shaida hakan akan kansu, Allah ma ya shaida hakan akan kansu, suka kuma isar da shi zuwa ga al'ummomin su cewa lallai wannan alƙawari ya wajabta masu yin imani da taimakon wannan Annabi, shin sun riske shi, ko ba su riske shi ba, sai ya zama dole ne al'ummomin su su yi imani da shi, su kuma taimake shi; saboda cika alƙawari da biyayyar da Annabawan su suka ɗauka)** [Ali Imran: 81].

Haka ma a cikinsu akwai: Irin yanda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ga "al- Baitul Ma'amur" a sama, Annabinmu

(SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Sai ga shi na ga Annabi Ibrahim ya jingina bayansa a "al- Baitul Ma'amur", sai na ga ɗakin a kullum mala'iku duba saba'in ne suke shiga cikinsa, ba kuma za su sake dawowa cikinsa ba)**, lallai Allah mai girma da buwaya ya rantse da wannan ɗaki a cikin Alƙur'ani mai girma saboda daraja, gami da girman da yake da shi, Allah mai girma yana cewa: **(Ina rantsuwa da Baitul Ma'amur)** [aɗ- Ɗur: 4].

Haka ma a cikinsu akwai: Irin yanda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya dangana da Sidratul Muntaha, wannan babban girmamawa ne da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), Allah mai girma yana faɗi cewa: **(Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa alihi wa sallam) bai yi ƙarya a abin da ya riga ya gani da idonsa ba. Shin ma wai ƙaryata Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa alihi wa sallam) za ku yi, kuna yi masa gardama akan abin da ya gani da idanunsa ƙiri-ƙiri?!. Lallai Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ga mala'ika Jibrilu (AlaiHis-Salãm) a sifar da Allah ya halicce shi a karo na biyu. A wani wuri da babu wanda ya sani sai Allah, wanda ya yi wa suna da "Sidratul-Muntahã" (magaryar tuƙewa). Ya kuma bayar da labarin cewa a wurin ne akwai aljannar Ma'awa. Lokacin da falalar Allah da ba a iya misaltawa ta lulluɓe wurin)** [an- Najmi: 11- 16].

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai tafiyar Isra'i da Mi'iraji wani babban girmamawa ne da Allah ya yi wa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), bayan ya fuskanci wasu wahalhalu, da jarrabawa, saboda haka sai Isra'i da Mi'iraji suka zama wata baiwa ce da ta yaye damuwa, ta kuma tabbatar da zuciya, ta kuma kwantar da hankali, Allah mai girma yana cewa: **(Ai da ma can duk wata wahala tana tare da sauƙi, tabbas lallai duk wata wahala tana tare da sauƙi)** [as- Sharhi: 5- 6].

Lallai Allah mai girma da buwaya ya nuna wa Annabinsa haƙiƙanin abubuwan da suke a gaibi, da sirrorin halittarsa, saboda ya sanar da shi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) cewa lallai yana tare da Allah mai girma da buwaya, yana kuma ƙarƙashin kulawarsa, alhairin Allah ya kai zuwa ga Imam al-Busairiy a lokacin da yake cewa: "An yi tafiyar dare da kai daga ɗaki mai alfarma zuwa ɗaki mai alfarma, kaman yanda tauraro ɗan dare goma sha huɗu yake tafiya a cikin tsananin duhun dare. Haka ka yi ta cigaba har sai da ka sami matsayin kwatankwacin baka- biyu, ba a iya riskar ba, ba ma a yi tunanin isa zuwa ga matsayinka ba. Gaba ɗayan Annabawa da Manzanni a wurin, sun gabatar da kai a kansu, irin gabatarwa da ake yi wanda ake yi hidima da mai hidimar yake yi.

**Ya Allah Ubangiji ka azurta mu da koyi da Annabinka (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) a duniya, ka kuma sanya mu cikin cetonsa a lahira.**